Kada ku zagi Iska, idan kuka ga abinda ba kwa so to kuce: Ya Allah mu muna roƙonKa daga alherin wannan iskar, da alherin abinda ke cikinta, da alherin abinda aka umarce ta da shi, kuma muna neman tsarinKa daga sharrin wannan iskar, da kuma sharrin abinda ke cikinta, da kuma sharrin abinda aka umarce ta da shi

Daga Ubayyu ɗan Ka'ab - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: "Kada ku zagi Iska, idan kuka ga abinda ba kwa so to kuce: Ya Allah mu muna roƙonKa daga alherin wannan iskar, da alherin abinda ke cikinta, da alherin abinda aka umarce ta da shi, kuma muna neman tsarinKa daga sharrin wannan iskar, da kuma sharrin abinda ke cikinta, da kuma sharrin abinda aka umarce ta da shi".

[Ingantacce ne] [Tirmizi ne ya ruwaito shi]

(Annabi) tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya yi hani da a zagi ko tsinewa iska, domin ita abar umarta ce daga Mahaliccinta, tana zuwa da rahama da kuma azaba, aibanta ta aibanta Allah ne Mahaliccinta, da fushi akan hukuncinSa, sannan tsira da amincn Allah su tabbata agare shi ya shiryar zuwa komawa ga Allah Mahaliccinta da roƙonSa daga alherinta da alherin abinda ke cikinta da alherin abinda aka aikota da shi, kamar zuwanta da ruwa da ɗaukar abinci (wata madatta ce da take ƙarfafa jikin mutum ko dabba) da makancinsa, da kuma neman tsarin Allah daga sharrinta da sharrin abinda ke cikinta da kuma sharrin abinda aka aikota da shi, kamar bata tsirrai da bishiyoyi da kashe dabbobi da rusa gine-gine da makamancinsa, kuma a cikn rokon Allah akwai tabbatar da ubudiyya ga Allah.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/5976